Abu Saleh Ya kasance yana Umartarmu idan dayan mu zai bacci ya kwanta akan bangaren sa na dama

An rawaito daga Suhail, ya ce: Abu Saleh Ya kasance yana Umartarmu idan dayan mu zai bacci ya kwanta akan bangaren sa na dama, sannan ya ce: "ya Allah Ubangijin Sammai da Kasa kuma Ubangijin Al-arshi Mai girma, Ubangijin kowa ne abu, wanda ya Kawayar iri da kuma kwallon Dabino, Kuma wanda ya saukar da Attausa da Linjila da Kuma Qur'ani, ina neman tsarinka daga Sharrin kowane abu da kai riko da makwankwadarsa, Ya Allah kaine na farko wanda babu wani kafinka, kuma kai ne na Karshen da babu wani a bayanka, kaine Sama da kowa wanda babu wani Sama da kai, Kaine boyayye wanda babu abu ba kai ba, Ka biya mana bashi, kuma ka wadata mu daga Talauci" kuma ya kasance ya rawaito wannan ne daga Abu Huraira, daga Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6335